MINISTÈRE
DE L'EUROPE
ET DES AFFAIRES
ÉTRANGÈRES
*Liberté*
*Égalité*
*Fraternité*

DIRECTION GENERALE DE L'ADMINISTRATION
ET DE LA MODERNISATION

DIRECTION DES RESSOURCES HUMAINES

Bureau des concours et examens professionnels

# CONCOURS EXTERNE, INTERNE ET 3ème CONCOURS POUR L'ACCÈS AU CORPS DES ADMINISTRATEURS DE L'ÉTAT DÉNOMMÉS « CONCOURS D'ORIENT » AU TITRE DE L'ANNÉE 2023

---

**ÉPREUVES ÉCRITES D'ADMISSIBILITÉ**

**Mercredi 7 septembre 2022**

# HAOUSSA

Durée totale de l'épreuve : 3 heures
Coefficient : 2
Toute note inférieure à 10 sur 20 est éliminatoire
Barème de notation : composition en haoussa 12 points ; traduction en français 8 points

**TRADUCTION EN FRANÇAIS**

*Traduction en français d'un texte rédigé en haoussa*

TEXTE AU VERSO

# Jihar Plateau : Magance rikicin manoma da makiyaya

Haɗin gwiwar ƙungiyoyin Fulani makiyaya a Plateau da ke tarayyar Najeriya, sun yi fatali da wata sabuwar doka ta haramta kiwon dabobi a bainar jama'a da majalisar dokokin jihar ke ƙoƙarin samarwa.
Ko da yake ya zuwa yanzu dokar haramta yin kiwon dabbobin a Plateau ba ta fara aiki ba, amma majalisar dokokin jihar ta yi wa dokar karatu na biyu. Tuni dai aka gabatar da ƙudirin dokar ga wani kwamiti da zai yi nazari a kanta kafin zama doka, kuma duk wanda ya saba ƙa'idojin dokar ya san akwai tanadin hukunce-hukunce da dama ciki har da biyan tarar maƙudan kuɗi. A dangane da haka ne haɗin gwiwar ƙungiyoyin makiyaya a Jihar ta Plateau ƙarƙashin shugabancin Nura Abdullahi suka yi fatali da ƙudirin dokar, sakamakon wasu dalilai.
Shi ma shugaban kwammitin sa ido game da sha'anin dokar a ɓangaren makiyaya, Isa Adamu Bappa, ya ce sun yi nazari kan ƙudirorin dokar, kuma sun lura idan ta fara aiki, za a kai ga cin zarafin makiyaya a Plateau kamar yadda yake faruwa yanzu haka a maƙwabciyarta Benue. Dangane da haka suke bai wa gwamnan jihar Simon Lalong shawarar ƙin rattaba hannu kan ƙudirin dokar.
Wasu daga cikin abubuwan da dokar ta tanada sun haɗar da cin tarar kuɗi da ba zai gaza Naira milyan daya ba, ko zaman gidan yari na shekaru biyar ga duk wanda ya karya dokar. Kazalika tilas sai makiyayan sun mallaki takardar shaida ta gwamnati kafin su iya mallakar wurin da za su killace dabbobinsu domin kiwo.

Kwanan wata 15.02.2022
Mawallafi Abdullahi Maidawa Kurgwi (AH/LMJ)
Permalink https://p.dw.com/p/4740Q